## Mene na musamman a wannan huduba?

Wa'yanda suka san Larabci ko akalla suna iya karatun rubutun Alkur'ani za su lura wasu harrufa na Larabci suna da digo tattare da su. Wa'yannan harrufa an irga su a kasan nan kuma ana amfani da su mafi yawan lokaci a zantukan Larabci da kuma rubutun takarda.

ش ب ت ن ض ث ق ف غ خ ج ز ظ ذ ي

Don a kirkiro rubutu mai ma'ana na ko wani iri, ba tare da an yi amfani da ko daya daga cikin wa'yannan harrufa ba, abu ne mai wahalan gaske. Don a bada irin wannan hudaba ba tare da wani shiri ba, yadda aka san Imam 'Ali (a) yayi a duk hudubobin sa, abun al'ajabi ne da gaske!
[**A lura**: Harafin da ke matsayin *taa marbutah* ana rubuta shi ba digo a rubutun Larabci na farko]

## Shin akwai irin wa'yannan hudubobi?

Imam 'Ali (a) ya ta'ba bada wani kyakkyawan huduba wanda bayyi da harafin *alif* !!

Wannan harafi na harrufan larabci ba shakka shine mafi aukuwa cikin harrufan da ake amfani dasu a yaren . In hada wasu 'yan jimloli masu ma'ana ba da diga ban a da wuya, to yaya bada huduba, wanin da keda dumbin hikima da kuma ninkin yawa kan wanda aka gani a wannan shafin,amma ba ayi amfani da *alif* ko daya ba!!

Wannan huduba ana kiran sa *al-Khutbah al-Muniqah* kuma masana musulmai da dama sun ruwaito shi. Daga cikin malaman Sunni da suka nakalto akwai:

- Muhammad b. Muslim al-Shafi'i, *Kifayat al-Talib*, p. 248
- Ibn Abi'l Hadid al-Mu'tazili, *Sharh Nahj al-Balaghah*, vol. 19, p. 140

## Yaya Imam 'Ali (a) zai cimma wannan?

Imam 'Ali (a) ya tsakuri fadin ilimin shi da kaifin balaga ta darajan dogon zamanshi da kusancin mu'amalan shi da Annabi Muhammad (s). Annabi (s), ta wahayi daga Ubangiji, shine tsotson dukan ilimi da hikima kuma malami na kololuwa ma Imam 'Ali (a).

**Don karin sani kan Islam na kwarai, yadda Annabi Muhammad (s) da yadda Imam 'Ali (a) ya yi bayani bayan shi, ziyarci:**

***http://al-islam.org/faq/***

*v1.0*

Annabi Muhammad (s) ya ce:

**Ni ne gidan hikima kuma 'Ali ne kofarta**

(*Sahih al-Tirmidhi*, (bugun Cairo), Kitab al-Manaqib, vol. 5, shafi na 637, hadith number 3723)

# Huduba Marar 'Digo

Ilimi, hikima da balagan Imam 'Ali b. Abi Talib (a) sananne ne wajen Musulmai na dukan mazhabobi. Misalin daya daga cikin kwarewan shi a harshen Larabci ta bayyana kanta a huduban da yayi kai tsaye wanda, in tana tsarin rubutun ta , ba ta da ko digo a cikinta !!

**هذه خطبة لأمير المؤمنين علي بن أبي طالب (ع) جميع حروف كلماتها خالية من ذكر "النقطة":**

**بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ**

الحمد لله الملك المحمود، المالك الودود، مصور كل مولود، ومآل كل مطرود، ساطح المهاد وموطد الأطواد، ومرسل الأمطار ومسهل الأوطار، عالم الأسرار ومدركها، ومدمر الأملاك ومهلكها، ومكور الدهور ومكررها، ومورد الأمور ومصدرها، عم سماحه وكمل ركامه، وهمل، طاول السؤال والأمل، وأوسع الرمل وأرمل،

أحمده حمدا ممدودا، وأوحده كما وحد الأواه، وهو الله لا إله للأمم سواه، ولا صادع لما عدل له وسواه، أرسل محمدا علما للإسلام وإماما للحكام، سددا للرعاع ومعطل أحكام ود وسواع، أعلم وعلم، وحكم وأحكم، وأصل الأصول، ومهد وأكد الموعود وأوعد، أوصل الله له الإكرام، وأودع روحه الإسلام،

ورحم آله وأهله الكرام، ما لمع رائل وملع دال، وطلع هلال، وسمع إهلال. إعملوا رعاكم الله أصلح الأعمال، واسلكوا مسالك الحلال، واطرحوا الحرام ودعوه، واسمعوا أمر الله وعوه، و صلوا الأرحام و راعوها، وآعصوا الأهواء وآردعوها، وصاهروا أهل الصلاح والورع،

و صارموا رهط اللهو والطمع، ومصاهركم أطهر الأحرار مولدا وأسراهم سؤددا، وأحلامكم موردا، وها هو إمامكم وحل حرمكم مملكا، عروسكم المكرمه، وما مهر لها كما مهر رسول الله أم سلمه، وهو أكرم صهر، و أودع الأولاد، وملك ما أراد، وما سهل مملكه ولا هم ولا وكس ملاحمه ولا وصم، اسأل الله لكم أحمد وصاله، ودوام إسعاده، وألهم كلا إصلاح حاله والأعداد لمآ له ومعاده، وله الحمد السرمد، والمدح لرسوله أحمد.

Dukan godiya ya tabbata ga Allah: Sarkin da ake wa godiya, Mamallaki mai tausayawa, mai Siffanta dukwanda aka haifa, wajen Komawa ga duk wanda aka zalunta, mai Buda filaye, mai Dasa dukan duwatsu, mai aiko ruwa, mai Sawwakke wahalhalu, mai Sani da kuma Gane asirrai, mai Ruguje masarautu da Rushe ababen da aka mallaka, mai Sabunta zamanoni da kuma Maimaitasu, mai Asalin komai da Makoman su. Kyautan shi ya fadada kuma jerin gajimaren sun isa da zuban ruwa. Yana kula da wanda ya tambaya ko ya sa kauna, yana ba wa kowa da kuma yawan gaske .

Ina maSa godiya ba karshe. Na dauke Shi daya yadda wanda suka koma gare Shi suka dauke Shi daya. Lo ! Shine Allah, ba wani abun bauta wa wa dukkan al'ummu sai Shi. Ba wanda ya isa ya jirkita abun da ya tsayar a mike kuma ya kafa. Ya tura Muhammad azaman alami na mikawa (*Islam*), da shugabancin masu mulki da kariya daga danniyansu, Mai gurgunta ikon *Wudd* and *Sawa`* (gumaka biyu). Mai sanarwa da ilimantarwa, kafawa da kammalawa. Shi ya samo asalin kuma ya kafa su. Ya nuna muhimmancin ranan alkawari (Ranan Kiyama) kuma ya yi gargadi. Allah ya dangana shi da karama kuma ya bawa ruhinsa kwanciyan rai, kuma Allah ya bada rahama wa zuri'an shi da mutanen gida masu daraja; muddin taurarin nuni suna haske, wata ya cigaba da ketowa, da kuma fadin kadaitaka (*La ilaha illa Allah*) ya kasance ana jin a ko ina.

Allah ya kare ka! Yi aiki zuwa ga mafi kyawun ayyuka. Saboda haka bi hanya kana neman halal, ka kuma bar abun da aka haramta ka kuma guje shi. Ka ji dokan Allah ka kuma kiyaye shi. Kula da zumuncin danginka ka kuma tsare su. Ka ki biyayya ga son zuci ka kore su. Ka hada zumunci da masu gaskiya da tsoron Allah, ka kuma yanke wa taron masu bin sha'awa da kwadayi.

Angon ku yana daga cikin mafi kyaun mutane masu 'yanci a haife, mafi kyautatawa da karama tare da tsarkinsu, da mafi dadin tsotso. Ya zo wajen ku, ya dauki 'yar'uwan ku, budurwa mai daraja da izinin ku, domin aure. Ya bada sadaki, yadda manzon Allah ya ba wa Umm Salamah. Hakika, shi [s] ya kasance siriki mai karama. Mai yin kirki ga zuri'an shi. Yan a bada su a aure ga wanda ya so. Baya cikin rudu wajen zabin mata kuma baya kallon gefe.

Ina rokon Allah, a madadinku, don rahaman Shi da baya yankewa. Da kuma ci gaban yardan Shi, dan Ya sanar da kowa: gyaran halin da suke ciki, da shirin makoman kowani daya cikin su da ranan kiyama. Godiya naShi ne har abada da kuma yabon Manzon Shi Ahmad [s].

**Wannan huduba yana kaman Imam 'Ali (a) ya yi shi a taron auren wani (*nikah*), kuma yana iya yiwuwa aurensa ne ma. Marubuta da yawan gaske sun nakalto shi a rubutun su kaman:**

- Muhammad Rida al-Hakimi, *Saluni qabl an tafqiduni*, vol. 2, pp. 442-3.
- Sayyid al-Musawi, *al-Qatarah min bihar manaqib Aal-Nabi wa al-`Itrah*, vol. 2, p. 179
- Hasun al-Dulafi, *Fada'il Aal al-Rasul*, p. 6